# Wasika Mai Nuna Yawan Kauna
Daga Wurin Allah Zuwa Gare Ku.

*Yaya Na,*

*Mai yiwuwa baku san ni ba, amma ni na san kome game da ku.* Zabura 139:1 *Da zaman ku da tashin ku duk na sani.* Zabura 139:2 *Na saba da duk al'amuran ku.* Zabura 139:3 *Har gashin kan ku ma duk a kidaye ya ke.* Matta 10:29-31 *Na halicce ku cikin siffa ta.* Farawa 1:27 *Ta gare ni ne kuke rayuwa, kuke motsi, kuke kuma kasancewa.* Ayyukan Manzanni 17:28 *Ku ma zuriya ta ce.* Ayyukan Manzanni 17:28 *Na san ku tun kafin a yi cikinku.* Irimiya 1:4-5 *Tun kuna ciki na maishe ku abin gado na.* Afisawa 1:11-12 *Ba ta hanyar kuskure na yi ku ba, kwanakin ku duka na rubuta a littafi na.* Zabura 139:15-16 *Ni na halicce ku, na kuma kayyade in da za ku zauna.* Ayyukan Manzani 17:26 *Yadda na yi ku abun banmammaki ne.* Zabura 139:14 *Ni na harhada ku a cikin mahaifan ku.* Zabura 139:13 *Tun da aka haife ku, ina kiyaye ku.* Zabura 71:6 *Wadanda basu san ni ba, ba za su gane maganata ba.* Yahaya 8:41-44 *Ba na nisa ko fushi, ina da cikakiyar kauna domin ku.* 1 Yahaya 4:16 *Ina marmarin nuna maku ainihin kauna.* 1 Yahaya 3:1 *Domin ku yaya na ne, ni kuwa Uban ku ne.* 1 Yahaya 3:1 *Ina ba da kyawawan kyautai fiye da ubanni na duniya.* Matiyu 7:11 *Ni ne Uba na kwarai.* Matiyu 5:48 *Kowace kyakkyawar baiwa daga wuri na ta ke.* Yakubu 1:17 *Dukkan komai nawa ne zan kuma biya duka bukatun ku.* Matiyu 6:31-33 *Shirin alheri ne na ke da shi domin ku.* Irimiya 29:11 *Ina kaunar ku da madawwamiyar kauna.* Irimiya 31:3 *Yawan kyakyawan tunani da nake da shi domin ku, in da za'a kidaya shi za ya fi yashin teku yawa.* Zabura 139:17-18 *Ina murna da ku ta wurin raira waka.* Zafaniya 3:17 *Bazan fasa nuna maku alheri ba.* Irimiya 32:40 *Ku zababbiyar jama'a ta che.* Fitowa 19:5 *Ina marmarin dasa ku a wanan kasa da aminchi da zuchiya daya.* Irimiya 32:41 *Ina so in nuna maku manyan al'amura masu girma da banmamaki.*Irimiya 33:3 *Idan kun neme ni da dukan ranku, za ku same ni.* Maimaitawar Sharia 4:29 *Ku nemi farin cikinku a wuri na, zan kuwa biya maku bukatunku.* Zabura 37:4 *Ni ne mai aiki a zuchiyar ku.* Filibiyawa 2:13 *Ina da ikon aikatawa fiye da yadde kuke tsammani.* Afisawa 3:20 *Ni ne mai ba da madawwamiyar ta'aziyya.* 2 Tasalonikawa 2:16-17 *Ni ne kuma Allah na dukan ta'aziyya.* 2 Korantiyawa 1:3,4 *Lokachin da kuna bachin zuchiya ko damuwa, ina kusa.* Zabura 34:18 *Zan rungume ku yadda makiyayi ke yi.* Ishaya 40:11 *Wata rana zan share maku dukkan hawaye.* Wahayin Yahaya 21:3-4 *Bakin ciki, da kuka, da azaba duk zan dauke.* Wahayin Yahaya 21:3- 4 *Ni Uban ku ne kuma ina kaunar ku yadda nake kaunar da na, Yesu.* Yahaya 17:23 *Ta wurin Yesu ne kauna ta take bayyanuwa.* Yahaya 17:26 *Shi ne ainihin kamanni na.* Ibraniyawa 1:3 *Ya zo ya nuna yana goyan bayanku. Baya gaba da ku.* Romawa 8:31 *Ba na lisafta laifofin ku.* 2 Korantiyawa 5:18-19 *Yesu ya mutu domin ya sulhunta ku da ni.* 2 Korantiyawa 5:18-19 *Mutuwar sa ta zama cikakkiyar bayyanuwar kaunar sa domin ku.* 1 Yahaya 4:10 *Na ba da komai nawa domin in kaunace ku.* Romawa 8:31-32 *In kun karbi kyautar da na Yesu, kun kuwa karbe ni.* 1 Yahaya 2:23 *Ba abu da zai sake raba ku da kaunar da nake da ita domin ku.* Romawa 8:38-39 *Akwai baban buki da za a yi a sama in kun zo gida.* Luka 15:7 *Ni ne Uba. Ni ne Uba har'abada.* Afisawa 3:14-15 *Tambayar ita ce… za ku zama yaya na?* Yahaya 1:12-13 *Ina jiran ku.* Luka 15:11-32

*Da yawan kauna, Uban ku Allah mai Tsarki*

Abba

Hausa Father's Love Letter © 1999 Father Heart Communications - FathersLoveLetter.com - Please feel free to copy & share with others.